

# AYI HATTARA,

## DAI WANNAN SHINE ADDININ SHIA

نسخة الهوسا

رامي عيسى

# WANNAN SHINE ADDININ

Muna godiya ga Allah Mai taimakon Sunnah da Musulunci da addini ta hannun ma'abota Sunnah. Muna yabo da salati ga Annabinmu Muhammad (s.a.w), da Iyalansa da Sahabbansa da wadanda sukayi kwaikwayo dasu har zuwa Ranar Qiyama. Bayan haka:

Lalle abu ne mai baqanta zuciya, kuma mai sa idanu suyi hawaye ganin cewa Musulmi masu yawa an yaudare su zuwaga addinin Shia Rafidawa. Har wasu suna tsammanin cewa banbanci tsakaninmu da yan Shia ba wani abu bane face banbacin fahimtar Fiqihu, irin wanda ake samu tsakanin Mazhabobin Ahlus Sunnah {guda hudu}. Saboda girman wannan al-amarin inason inyi bayanin (wasu daga cikin) abubuwan da suke boye daga yawancin Musulmi.

# DAN UWA MUSULMI KASAN CEWA:


SHIA RAFIDAWA NA CEWA BASU BAUTAMA ALLAH MU!???
Babban Malanin Shia Ni'imatullah al-Jaza'iri yace: "Bamu tarayya dasu – yan Ahlul Sunnah – akan Ubangiji daya ko Annabi daya ko Imami (Shugaba) daya. Saboda su suna cewa: Lalle Ubaganjinsu shine wanda Muhammad ya kasance Annabinsa, kuma kalifansa, bayan rasuwarsa shine Abubakar. To mufa bamu iqrari da wannan Ubangijin da wancan Annabin. Lalle Ubangijin da yake kalifan Annabinsa Abubakar ba Ubangijin mu bane, kuma wancan Annabin ba Annabinmu bane." (Dubi littafin AL-ANWAR AN-NU'AMANIYYAH, sihili na 1, shafi na 278).
Wannan maganar na tabbatar maka da cewa Shia basu bautama Allah Ta'ala. Su suna bautama Allan da Ubanganjinsa ba Annabi Muhammad (s.a.w) bane.



# SHIN KASAN CEWA:

YIN IMANI DA CEWA AL-QUR'ANI BA CIKAKKE BANE NADAGA CIKIN SHARUDDAN ZAMA DAN SHIA

Babban Malamin Shia wanda ake kira al-Mufid, wanda suke cewa wai Imam Mahdi ne ya bashi wannan laqabin saboda ya kirashi da: "Dan uwa ma daidaici, kuma masoyi shiryaiye." Wannan Malamin nasu ya tabbatar dacewa dukansu sunyi Ijma'i akan an canza al-Qur'ani.
Ga abinda yake cewa: "Yan Shia Imamiyyah sunyi ittifaqi akan aqidar Raj'ah (dawowa duniya bayan mutuwa domin ayi sabuwar rayuwa), kuma sunyi ittafaqi akan cewa Shugabannin bata (watau Abubakar, Umar da Usman) sun kawo canji mai yawa a wurin tara al-Qur'ani kuma sun karkatar dashi daga yadda aka saukar dashi da Sunnar Annabi (s.a.w)." (Dubi littafin AL-AWA'IL AL-MAQALAT, shafi na 52).
Babban Malaminsu al-Nur al-Tabarsi, wanda suke yima laqabi da Malamin Malammai ya rubuta littafi mai suna FASLUL KHITAB FI TAHRIF KITAB RABBUL ARBAB (Rarrabewar Magana akan canza littafin Ubangijin talikkai). Ya anbata a cikin littafin cewa hadisan-su da riwayoyinsu sahihai fiye da dubu sun tabbatar da cewa an canza al-Qur'ani. Wadanda ke inkarin wannan maganar daga cikin Malamman Shia sunayi ne domin taqiyyah, don kada sauran Musulmi su gane cewa wannan haqidar, tabbatar gaskiya ce a wurin su.



# KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA SUNA DA'AWAR CEWA ANNABI YA KASANCE YANA SHAN NONON KAWUNSA ABU TALIB!???

Babban Malamin Shia al-Kulaini, wanda sukeyima laqabi da yardadde a Musulunci, ya ruwaito a cikin littafin sa al-kafı (shine Sahihin littafin su na hadisi), cewa Abu Basir yace, Abu Abdullah yace: "Bayan an haifı Annabi (s.a.w)... ya rayu na yan kwanakki bayada nono. Sai Abu Talib ya miqa masa nonon sa. Sai Allah Yasa ruwa ya dinga fıtowa daga nonon sa. Ya rinqa baiwa Annabi nono na yan kwanakki kafin ya miqa-shi zuwa hannun Halima as-Sa'adiyyah." (Dubi al-Kafı, sihili na 1, shafı na 448).



# KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA SUNA TUHUMAR MALA'IKU DA SABON ALLAH KUMA SUNA FUSHI DA ALI BIN ABI TALIB

Babban Malamin yan Shia Abu Ja'afar as-Saffar wanda sukeyima laqabi da babban amintacce da fitaccen Malamin hadisi, ya rubuta a cikin littafinsa mai suna BASA'IR AD-DARAJAT (shafi na 68), cewa Imam Abu Abdullah yace: "Lalle Allah ya gitta (Imamah) Shugabancin Ali bin Abi Talib ga Mala'ikku sai suka amince da ita face dayansu wand ake kira Fitris. Saboda haka Allah Ya karya fikafikansa."

(Amma ku Musulmi kun sani) Allah Ya gaya mana dangane da Mala'iku cewa: "... basu saba wa Allah ga abin da Ya umurce su, kuma suna aikata abin da ake umurmin su." (Suratul Tahrim: 6).



# KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA NA DA'AWAR CEWA IBLIS YA KASANCE YANA SON ALI BIN ABI TALIB KUMA YANA KARESHI!??

Babban Malamin Shia as-Sadouq, wanda suke kira limamin zamanin sa ya ruwaito cewa Imam Ali yace: "Nabi bayan la'anne (Shedan), dana cimmasa, sai na kama shin na kayarda shi, na dora hannuna akan wuyan sa domin in shaqe shi. Sai yace: 'Kada ka aikata wannan ya baban Hasan. Lalle ina cikin wadanda aka yima jinkiri (sai Ranar Qiyama). Ya Ali Wallahi lalle ina sonka qwarai. Kuma duk maqiyin ka nayi tarayya da mahaifin sa lokacin da yake jima'i da uwar sa. Don haka dan zina ne.' Sai nayi dariya na qyaleshi." (Dubi littafin UYUN AKHBAR RIDA, sihili na 1, shafi na 77).



# KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA NA CEWA MUTUN BAYA KASANCEWA DAN SHIA SAI YA LA'ANI SAHABBAN MANZON ALLAH DA MATAN SA, KUMA YA BARRANTA DAGA GARESU!!!

Babban Malanin su Baqir al-Majlisi, wanda sukeyima laqabi da abun al-faharin al-Ummah da Malamin Malammai, ya rubuta cewa:
"Aqidar mu dangane da Annabci itace: "Lalle mun barranta daga gumaka hudu: Abubakar, da Umar da Usman, da Mu'awiyyah, da matan sa hudu: A'isha, da Hafsa, da Hind, da Um al-Hakam, da dukan mabiyan su da magoya bayan su. Kuma lalle sune mafi sherin halittun Allah a doron qasa. Kuma lalle Imani da Allah, da Manzon sa, da Imamai baya tabbata sai bayan an barranta daga maqiyan su." (Dubi littafin HAQQUL YAQIN, shafi na 519).
Kuma al-Majlsi yayi da'awar cewa: "Fir'auna da Hamanan wannan al-Ummar sune Abubakar da Umar." (Dubi littafin BIHAR AL-ANWAR, sihili na 3, shafi na 41).



# KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA NA CEWA DUK LOKACIN DA SAYYIDUNA ABUBAKAR KEYIN SALLAH BAYAN MANZON ALLAH AKWAI GUNKI A RATAYE A WUYAN SA KUMA GUNKIN YAKE YIMA SUJUDA!???

Shugaban Malamman Shia, Ni'imaullah a-Jaza'ri yace: "Kada kuyi mamakin wannan hadisin. Lalle wata riwaya tazo a cikin riwayoyin mu na musamman cewa Abubakar ya kasance yana Salla bayan MAnzon Allah, yana mai rataye da gunki a wuyan sa, kuma ya kasance yana yi masa sujuda." (Dubi littafin ANWAR AN-NU'UMANIYYAH, sihili na 1, shafi na 53).



# KO KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA NA DA’AWAR CEWA SAYYIDINA UMAR ZAIFI SHEDAN SHAN AZABA A WUTAR JAHANNAM!???

Babban Malamin su Ni’imatullah al-Jaza’iri yace: “Yazo a cikin riwayoyi mu na musamman cewa za’a daure Shedan da ququmi saba’in na wutar Jahannama, sai a jawo shi zuwa wurin hisabi, sai yaga wani mutun Mala’iku na jaye dashi kuma a wuyan sa an sa masa ququmin Jahannama dari da ishirin. Sai Shedan yazo kusa dashi yace: ‘Me wannan shaqiyin ya aikata har yafini shan azaba, gashi kuwa nine na batar da dukan mutane, kuma na tura su zuwa wuraren halaka? Sai Umar yace ma Shedan: ‘Ban aikata wani laifi ba face na karbe shugabancin Ali bin Abi Talib.’” (Dubi litafin ANWAR AN-NU’UMANIYYAH, sihili na 1, shafi na 18-28).



# KO KA SAN CEWA:

MALLAMAN SHIA NA TUHUMAR SAYYIDUNA USMAN – WANDA SHI ANNABI YA AURAR MA DIYAN SA GUDA BIYU, BAYAN TA BIYUN TA RASU SAI YACE DA AKWAI TA UKKU DA NA AURAR DA ITA GA USMAN – MALAMMAN SHIA SUNA CEWA KAFIRI NE MUNAFIQI!???


Babban Malamin su Ni'imatullah al-Jaza'iri yace: "A zamanin Manzon Allah (s.a.w), Usman ya nuna shi Musulmi ne amma Munafiki ne." (Dubi littafin ANWAR AN-NU'UMANIYYAH, sihili na 1, shafi na 81).
Bayan haka kuma sun wajabtar ma yan Shia kafirtadda Usman da zagin sa. Wani Malamin su al-Kurki yace: "Lalle duk wanda baya qiyaiya da Usman, kuma baya zagin sa kuma baiyi Imani da cewa kafiri ne ba. To lalle wannan mutumen maqiyin Allah ne da Manzon Sa kuma ya kafirta da abinda Allah Ya saukar." (Dubi litafin NAFHAT AL-LAHOUT, shafi na105).



# KA SAN CEWA:

IMAM ALI BIN ABI TALIB BAI TSIRABA DAGA SUKAR YAN SHIA!!!?

Malamman Shia sunce Imam Ali shine sauro a cikin tafsirin wannan ayar: “Lalle ne, Allah ba Ya jin kunya Ya baiyana wani misali, kowane iri ne, sauro da abinda yake bisa gare shi…” (2:26). Sai babban Malamin su al-Qummi yace wai Imam Abu Abdullah yace: ‘Abunda ake nufi da sauro anan shine Ali bin Abi Talib, abinda ke bisa gareshi kuwa, shine Manzon Allah (s.a.w).’” (Dubi Tafsir al-Qummi, sihilina 1, shafi na 34). Malamin Hadisin su as-Shirazi yayi sharhi akan wannan hadisin yana mai cewa: “Wannan riwaya ce mai daraja. Lalle Ali bin Talib sauro ne.”






# KO KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA SUNA YIMA A'ISHA MATAR MANZON ALLAH QAZAFIN ABINDA ALLAH YA WANKE TA DAGA GARESHI!!??

A wurin tafsirin wannan ayar: "Allah Ya buga wani misãli dõmin wa□an-da suka kãfirta: mãtar Nũhu da mãtar Lũ□u, sun kasance a □ar□ashin wasu bãyi biyu daga bãyinMu sãlihai, saisuka yaudare su, sabõda haka ba su wadãtar musu da kõme daga Allah ba. Kuma aka ce: "Ku shiga, kũ biyu, wutã tãre da mãsu shiga." (66:10). Al-Qummi da al-Majlisi suka ce: "Wallah abind ake nufi da 'suka yaudare su,' aikata alfasha. Kuma dole ayi haddi zina akan WANCE – yana nufin A'isha, akan hanyar zuwa Basarah." (Dubi TAFSIRUL QUMMI, sihili na 2, shafi na 377). Yana nufin idan Mahadin su yazo sai tayarda A'isha daga qabarin ta yayi mata haddin zina kamar yadda suke da'awa. Allah Ya wulaqanta su.

Wani Malamin su wanda ake kira Rajab al-Bursi yace: "Sayyidah A'isha ta tara Dinari arba'in daga aikin alfasha, kuma ta rarrabar da kudin ga maqiyan Ali bin Abi Talib." (Dubi litafin MASHARIQ AN-WAR AL-YAQIN, shafi na 86). Rafidawa nayi mata laqabi da fajira, kamar yadda suke fada a tashar telibijin ta FADAK, da wasu wuraren.
To kai ka yarda da wannan mugun nufin ga uwar Muminai A'isha (r.a)???



# KO KASAN CEWA:

SHIA RAFIDAWA SUNYI IMANI DA CEWA ABUBAKAR, UMAR, A'ISHA DA HAFSA SUNE SUKA KASHE MANZON ALLAH (S.A.W)!!??

Shehun Malamin su Al-Ayyashi wanda suke yima laqabi da babban Malanin hadisi, ya anbata a cikin tafsirin sa cewa; Imam Abu Abdullah yace: “Ko kun sani, Annabi ya rasu ne ko an kasheshi ne? Allah Yace a cikin al-Qur'ani: ‘Kuma Muhammadu bai zama ba face manzo lalle ne manzanni sun shũ⊠e a gabãninsa. Ashe idan ya mutu ko kuwa aka kashe shi, zã kujũya a kan dugaduganku?...’ (3:144). Sai aka bashi guba kafin ya mutu, sune suka bashi guba; A'isha da Hafsa. Saboda haka muka ce; dasu da mahaifan su sunfi kowa sheri a cikin halittun Allah.” (Dubi Tafsirul Ayyashi, sihili na 1, shafi na 200).
Al-Majlisi yace: “Lalle Ayyashi ya ruwaito hadisi mai isnadi ingantacce daga Imam Sadiq cewa A'isha da Hafsa da uwayen su, sune suke kashe Manzon Allah ta hanyar shayar dashi guba. Sune suka shirya makircin,” (Dubi littafin HAYATUL QULUB, sihili na 2, shafi na 700).



# KO KASAN CEWA:

MALAMMAN SHIA NA DA'AWAR CEWA DUK YAN AHLUS SUNNAH DIYAN ZINA NE!!!???

Babban Malamin su, wanda suke yima laqabi da yardad-den Musulinci, al-Kulaini a cikin litafin sa al-Kafi (sihili na 8, shafi na 285): "Dukan mutane diyan karuwai ne face yan Shia'armu."



# KO KASAN CEWA:

MALAMAN SHIA SUNYI IMANI DA CEWA ZIYAR QABARIN HUSAINI A RANAR ARAFA YAFI AIKIN HAJJI DA UMRAH SAU MILIYAN!!???

Babban Malamin su Hur al-Amili ya ruwaito cewa Imam Sadiq yace: “Duk wanda ya ziyarci qabarin Husaini ranar Arafa Allah zai rubuta masa ladar aikin Hajji miliyan tare da Imam Mahadi, da ladar aikin Umrah miliyan tare da Manzon Allah (s.a.w), da ladar yantar da bawa dubu, da ladar bayar da doki dubu saboda Allah. Ubangiji zai kirashi da sunan Siddiq, wand yayi Imani da gamuwa dani. Mala’iku zasuyi shelar cewa wane Siddiq ne, Allah Ya bashi wannin sunan daga saman al-Arshin Sa.” (Dubi littafin WAS’IL ASH-SHIA, sihili na 1, shafi na 39).
Wannan wani qoqarine suke yi na jaye mutane daga aikin Hajji zuwa ziyarar qabarin Husaini a garin Karbala.

Republished by: www.shafaqna.com




# KO KASAN CEWA:

YAN SHIA SUNYI IMANI DA CEWA DUK MAHAJJATAN DAKIN ALLAH ALADDU NE DA BIRAI FACE RAFIDAWA!!!???

Babban Malamin su Abu Ja'afar as-Saffar ya ruwaito cewa, Abu Basir yace: "Nayi aikin Hajji tare da Abu Abdullah, a lokacin da mukeyin dawafı, nace masa: 'Allah Ya yantar da kai, yakai dandan Manzon Allah! Allah zai gafarta ma dukan wadannan mutane?' Sai yace: 'Yakai Abu Basir! Yawancin wadanda kake gani aladdu ne da birai.' Sai nace masa: 'Gwada mani su.' Sai yayi wasu maganganu, kuma yabi da hannunsa akan idanu na. Sai nagan su birai da aladdu, wannnan al-a'arin ya bani tsoro. Sai ya sake bida hanun sa akan idanuwa na, sai nagan su kamar ganin farko.'" (Dubi littafin BASA'IR AD-DARAJAT, shafi na 260).

www.rafqiyal.org



# KOWA YA KAMATA YA SAN CEWA;

1. Abubuwan da muka ambata a sama abubuwa ne masu nauyi sosai na sheri da mugunta da mugunyar qiyaiya. Muna kai kukan mu ga Allah. Babu qarfi ko wata dubara sai da taimakon Allah Madaukaki, Mai Girma. Allah Ka yarda da dukan Sahabban Manzon Allah da Uwayen Muminai.

2. Wadannan littafan da muka ambata a sama sune wadanda yan Shia suka yarda dasu kuma sun dauki marubatan su Malanman su da abun koyin su, suna girmama su, suna yabon su, kuma suna yima su addu’o’in fatar alheri.

DAGA QARSHE: KANA GANIN YAN SHIA RAFIDAWA MUSULMI NE?



Autor : **Rami Isa**

+201111012626

RAMY_EASA2016

t.me/RAMYESSA_HAUSAA

fb/Rami-Isa-Hausa-103860947932108



www.islamic-invitation.com